An sa mana lokaci a rage gashin baki, da yanke farata, da cire gashin hammata, da aske gashin mara, kada mu bari sama da dare arba'in

Daga Anas ɗan Malik - Allah Ya yarda da shi - ya ce: An sa mana lokaci a rage gashin baki, da yanke farata, da cire gashin hammata, da aske gashin mara, kada mu bari sama da dare arba'in.

[Ingantacce ne] [Muslim ne ya rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya iyakance akan rage gashin bakin namiji, da yanke farcen hannaye da ƙafafuwa, da cire gashin hammata, da aske gashin mara, cewa kada a barsu sama da kwanaki arba'in.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/66049